**USULAR KIWON LAHIYAR JAMA 'A**

Kahin –Bayani

Lahiya na da nassaba ga al'uma,da tattalin arziki da kuma siasar kassa.Talauci,zalumci,hin karhi da rashin aiki da gaskia,sune ke hadassa mutuar mutane marassa abin kan su har ma da aihuatar cuta ga warenrun mutane.Samun cikakar lahiya ga kowa,na iya wakana idanan tanadi manyan mukarabai,da kuma kawo sauyi ga abubuan da siasa tare tattalin arziki su kumsa.

Wan'nan usula,an kirkiro ta,bisa zaton maza da mata,waden da,ba a saba jin muryar su ba a da.Ta na kara ma jama'a karhin bunkassa dubarun su,da kuma tilassawa ma magabatan jahohi,na kassa ko na kasashe da kasashe da su yi aiki kan nauyin da ya rataya a gare su.

Hangen Nesa

Rashin cin zali da zaman lahiya,game da kiyaye daji(da abin da daji ya kumsa),shi ne mu ke hange domin kyewtata rayuar mu a duniya.Ya kasance ba wata matsala ga rayua,ga kuma abin da ya shahi rayua ;yadda muryar jama'a na iya kawo sauyi,da kuma dauken sabin matakan da ke iya kawo sauyi ga rayuar su.Akwai ishashen halin da ke iya bada damar cinma wan'nan guri.

**Tabarbarewar Kiwon Lahiya**

« Gare mu ,cuta da mutua na zaman babban abin da ke damun mu dare da rana.Ba dan mutane na rashin lahiya ko mutua ba,dan dai yawancin cutar da mutuar na da nassaba ne ga muguar siasar da a ka tilasawa jama'a tare da mugun tattalin arziki »

(Muryar America ta Tsakia)

Sauye-sauyen tattalin na ko ina a shekarun baya ya haddassa koma bayar kiwon lahiyar jama'a,da kuma kawo cikass ga samun damar lara da makaraben kiwon lahiya.

Duk da ganin karuar arziki daban daban cikin duniya,talauci da yinwa sai karua su ke.Ramin da ke tsakanin kasashe ma su talauci da ma su hannu da shuni,sai karua ya ke shi ma.Haka kuma,banbanci tsakanin al'umomi,ko tsakanin maza da mata,yara da manya,ya na ci gaba.

Yawancin jama'a na fama da rashin abinci,ga ba horo,ga rashin kyew-kyawan ruan sha,da mazamni.Akwai kanencin gonakan nomawa tare da rashin kadakadarin kiwon lahiya.

A na tono arzikan cikin kassa a gaugauce,ga an falma daji da abubuan da ya kumsa.Yin hakan na gurbatar da sansanin sararin samania wenda ya kumshi iskar da mu ke shaka,da ruan da mu ke sha tare da bisashen mu da kuma sauren halittu.A takaice,yin hakan,na kawo matsala ga duk wata rayua,misali ma ta kasashen da ba su da arziki.Rikici na karua,lokacin da wasu ke kirkiro makaman kare dangi .

Arkin duniya ,na komawa hannun tsirarun mutane,waden da ke cin moriar su su kadai.Haka kuma,tsiraru,ma su karhi da milki,su ke dauken matakan siasar tattalin arziki game da kungiar bankin duniya,da kuma kungiar kasuanci.Duka waden nan al'amura na aihuatar da matsaloli bisa rayuar da kuma kiwon lahiyar mutane gusum da arewa.

Akasarin ma'aikatun jama'a ba su iya shawo kan matsaloli da dama,sabili da ragewar kayan aiki.Hakan na wakana a lokacin da gwamnati ke rage gwargwadon dukiar da ya kamata ta bayar domin bian bukatar al'uma. Shan magani ga ma'aikatun kiwon lahiya na jama'a,ya zamana sai ka na da hali,sai wane da wane,ga kuma babban banbancin da ke akwai tsakanin ma'aikatun birni da na kauye.Jama'ar kauye ba ta samun bian bukata,sai sun bakunci birni.

Ma’aikatu ma su zaman kan su(na pannin kiwon lahiya)na kawo cikass da kuma rudani ga ma’aikatun kiwon lahiyar jama’a.Su na kuma sa mutane kewaye ma’aikatun domin rashin bian bukatu.Yin hakan na sa matalauta halin kaka ni ka yi,domin ba su da kudin ziartar ma’aikatun ma su zaman kan su.Yawancin cutocin da a ke iya warkar wa,kamar zazzabin cizon sabro,babban tari ;da kuma ciwon zamani(sida),sun zamana shedu ga rashin dauken niya ga gwamnatoci,domin shawo kan wan’nan matsala.

**<u>Ka’idodin Usula Pannin Kiwon Lahiya</u>**

-Samun cikakkar lahiya da rayua me kyew,yen-ci ga duk dan adam,wanda baya da nassaba da banbancin kabila,yaro ko tsoho,namiji ko mace,me hali ko talakka.

-Ka’idodin kiwon lahiya,kamar yadda mahawarar Alma Ata ta bayana a shekara dubu daya da dari tara da saba’in da takwass(1978),su kasance gindingirimin duk wata siasar kiwon lahiyar jama’a.Tun yanzu ya kamata a dauki niyar da ke da yawan hussa’a,me kuma bada damar kawo gudumua.

-Gwamnatoci,su dauki nauyin samar da hanyoyin da ke iya kawo larar yen kassa ga kiwon lahiya,da kuma samun horo,ko yin anfani da sauren ma’aikatu.Yin hakan na bada damar sanin gwamnatin ya yi domin bian bukatun yen kassa,ba wai saboda abin da jama’a za ta bia ba.

-Gudumuar mutane da kungioyi,na iya bada damar kirkiro, da kuma sarafa siasar kiwon lahiya,ko girkar da wasu ma’aikatun da ya kamata jama’ar ta dace.

-Kiwon lahiya na tahia tare da  al’amuran siasa,da na tattalin arzikin da kuma yadda al’umar ta kasance(koshin lahiya).Saboda haka,ya kamata ,ma su fadi a ji,na kawani sashe(gari,gunduma, jamhuria,kasashe ),da su dauki wan’nan guri tamkar na farko daga cikin waden da suka wajaba.

**Kira na dauken matakai :**

Ya cincinta mu dauki mattakai a kowani panni, sabili ga tabarbarewar kiwon lahiya a duniya.Matakan,na iya huskantar mutun guda,gunduma,jamhuria zua kasashen ketare. Matakan da za mu dauka tamkar girki su ne :

-**lahiya,yen-ci ne ga duk dan adam ; rashin zalumci da shara'a a kan gaskia na bada haske ga yanda matsayin kiwon lahiya ke huskanta tare da al'uma.Cikeken kiwon lahiya game da baiwa kowa yen-ci shi, su ne mu ke fatan ganin an kare a cikin yanayin siasa ko na tattatalin arzikin kassa**

Wan'nan usula na kiren jama'a dan :

- bada goyon baya ga duk wani kokarin samar da yen-ci a pannin kiwon lahiya.
- tilassawa gwamnatoci da kugioyin kasashe da kasashe ,da su kawo sauyi ga siasar kiwon lahiya da kuma yadda za a kare yen-cin dan adam a kowani panni.
- yen kassa, su zan ki matsawa gwamnati da, ya kasance, kare yen-cin dan adam da karhua-hua kiwon lahiyar jama'a, na cikin kundin dokar kassa a ko yaushe.

**Hare haren da a ke kaima makaraban kiwon lahiya:**

- alwashin tattalin arziki

**tattalin arziki na hanzalta kyew-kyawen kiwon lahiya.Ingarceciar siasar tattalin arziki na kare yen-cin dan adam da kuma kyewtata rayuar jama'a.**

- muguar siasar da a ka tilasawa gwamnatoci (a pannin fassalin kudi, noma ) tare da campanai ma su zaman kansu (ma su yi dank an su, ma su akwai dank an su) na gurguntar da rayuar jama'a.
- kasashen duniya da dama,missali ma su arziki,na anfani da arzikin su yadda su ke so,ta kowace hanya.Ba su aiki da abin da dokar tattalin arziki ta tsaida.Haka

kuma,wasu kasashen na anfani da sojoji domin karhua-hua zaman su a kasashe,tare da halakar da mutane.

Wan'nan usula na kira ga mutane domin su :

- tambaya ga kungiar duniya ta kasuanci da sauren kungioyi,da su daina take yen-cin al'uma da na tattalin arziki tare da yen-ci kiwon lahiya. Ya kamata su yi abubuan da ya dace domin kare kiwon lahiyar jama'a. A kawo sauyi a sashen milkin massanan da ke dauken matakan shirin gudanar da kasuanci.
- tambaya domin shahe bashin kasashen da ke farfadauwa.
- tambaya domin kawo cenji ga umurnin bankin duniya,da ma su fassalin kudin duniya,da su zan ki bada haske su kuma karhua-hua bin doka(yen-ci) game da bayar da riba ga kasashe ma su tasauwa.
- tambaya wajen campanai kasashe da kasashe,das su kiyaye gurbatar da lahiyar mutane,da kwarar ma'aikata. Ya kuma kasance ,ba su kawo matsala ga kassa(sararin daji da abin da daji ya kumsa ,da sararin samania)
- gwamnatoci,su tsaida dokokin tahiar da ayukan gona domin anfanin yen kassa,ba wai saboda yen kasua ba. Yin hakan na bada damar samun isheshen abinci,wanda ke sa yen kassa su lara .
- gwamnatoci,su dauki matakan kare yen-ci kiwon lahiyar jama'a,da kuma dokar kare yen –cin massana.
- tambaya domin duk wata hada hadar kudi tsakanin kasashe da kasashe,ta dogara kan ka'idar doka.
- ya kasance duk wata siasar tattalin arziki na dogara da bincike,wanda zai bada haske bisa abin da ke farua wajen pannin kiwon lahiya, da kuma binciken ganin

al'amura na tahia bisa ka'ida ,ba zalumci , ba banbanci tsakanin mace ko namiji.Ya kamata siasar ta kumshi matakan da ke iya bada damar gaskantar da waden nan al'amura.

- a yi watsi da lissahin kawai na tattalin arziki,(wanda a ke yi bisa zaton samun riba kawai ba wai domin karuar yen kassa ba, ko kuma bisa yenayin girma ko karuar mutun ga nauyi ,tsawo).Duk wani lissahin tattalin arziki na kira da a kare sansanin sararin samania, da sansanin daji da abin da daji ya kumsa, domin kare lahiyar jama'a. Siasar na kokarin bunkassa aikin kai da kai tamkar gudumua missali ma kamar aikin da ya ke bako ga mata.

Alwashin al'uma game da kyew-kyawar sisa :

- Kyew-kyawar sisa ga al'uma na kyewtata rayuar jama'a,da kuma halayen da su ke ciki. Mayar da tattalin arzikin kassa ga sunan duniya,da saide-saiden ma'aikatun jama'a,da kuma halayen ma'aikatu ma su zaman kan su , sharatsi ne ga al'uma,ga iyalin su, har ma ga al'adun sun a galgajia. Mata,na taka rawar a zo a gain a cikin kowace al'uma; amma ya kasance a na cid a hakin su, a na kuma mancewa da su tare da take yen-cin su ga yawancin bukatun su.
- Campanoni da ma'aikatu na jama'a na ci baya.Yawancin nauyin da ya rataya a kan su,sun koma hannun wasu campanai ma su zaman kan su (entemprise) . Waden nan campanan,ba su baiwa jama'a haske ko bayani bias abubuan da ke gudana.An kuma gano da cewar , ikon da wasu magabatan siasa,da kungioyi ma'aikata ked a shi sun zamana yen kalilan (ragag'gu), sa'idin da ma su karfin handama ke ci gaba da gudanar harkokin su yadda su ke so. Ya cencenta,democratia ta ja gaba cikin shirye-shiryen siasa da kuma bias abin da ya

rataya  ga duk yen kasssa. Akwai bukatar bunkasssa da kuma karhua-hua dauken niya cikin haske.

Wan’nan  usula na kira ga mutane da :

- su tambaya,su kuma bada goyon baya ga farfadauwar siasar da ke baiwa mutane dammar kawo ta su gudumua.
- samo hanyoyin  da ke shahe duk wani banbanci, tsakanin maza da mata; da samun damar ba kowa yen-cin shi domin zabben addinin shi,da bada ra’ayi,samun horo,rayua cikin zaman lahiya da lumana da kuma rashin nuna banbancin kabila wajen aiki.
- a matsawa gwamnatoci da su  girka dokar da za ta kare ,ta kuma bunkassa yen-cin kananen al’umomi tare da samun cikakkar lahiya.
- ya kasance,bada horo da kuma hanyoyin kiwon lahiya,sun e na farko cikin kundin siasa.Wan’nan usula na tambaya da a baiwa  yara da manya horo,missali ma horon yaran mata da mata ba tare da sun bia diya ba. A fara ba yara horo kahin shigar su lacole
- a tambaya  domin ma’aikatun jama’a su kasance ma su iya kiyaye kiwon lahiyar jama’a ne, kuma na kyewtata rayuar su a pannin kiwon lahiya(shan magani ga yara, rabon abinci, samara da matsugunni ga waden dab a su)
- da,a kar a bada goyon baya,a yi kuma watsi da duk wani tsarin siasar da ke iya tilasawa jama’a barin gidan su manomin su da kuma karkarar su.
- a kiye ma duk wani ra’ayin yen handama wanda ke kawo sharatsi ga yen-cin jama’a,missali ma ga rayuar mata da yara da kuma kananen kabilu.

- a yi watsi da damar da ke haddassa yawon bude ido domin karuanci da kuma fataucin mata da yara.

Alwashin sararin samania da na daji:

Gurbacewar ruan shad a iskar da mu ke shaka, da sauye-sauyen yana'yin lokaci nan da nan,ga kuma makaraban makaman nuclea tare da dattin su,da wasu maganan kasha kwari da kasha-kashen itace, na kawo miagun hatsari ga pannin kiwon lahiya da rayua me kyew.

rashin bin kadun waden nan mukarabai,da kuma anfani da su ba bisa ka'ida ban a samo tushe ga bian bukatun kasashe ma su arziki

Wan'nan usula na kire ga mutane,domin:

- campanai ma su zaman kan su da ma'aikatun jama'a,da sojoji, da su kiyaye duk kassahin da ke iya lalata sansanin sararin samania da kuma na daji,ya kasance sun danganta ga dokokin da siasar shirin ta kaiyade.
- gamnatoci,su rage bada damar anfani da gas hiye ga yadda rajejeniyar kasashe da kasashe ta ambata. Yin hakan ,na yiyuwa idan an kiyaye bin mugayen dubaru.
- a yi watsi da duk wata niyar ,ko ra'ayin girka campanai da ke iya gurbatar da lahiyar jama'a.
- a rage zari, da kuma irin halin rayuar da ke hallaka jama'a gusum da arewa. A tilassawa kasashen da ke irin waden ga mugayen campanai ma su guba, da su rage sarafe –sarafen su kashi tassa'in bisa dari.
- da, a samo hanyoyin da su kare ma'aikata tare da lahiyar su,da kuma ba su damar kasancewa cikin dauken matakan tahiar da aikin.
- da, a samu hanyoyin da su kare hatsarin wurin aiki,da na gida ko kuma na al'uma

- kar a bada goyon baya ga dubarun saida na mu sanni domin anfanar da wani ko wasu.Ya  kamata mu kare arzikan mu da kuma al'adun mu na galgajia
- ya kasance mutane ko al'umomi,na zaman kyew-kyawen magwadi, domin sannin abubuan da ke kai da kawo a kowani panni.Ya kamata a bukassa al'amuran da ke kawo haske kan yanayin tahiyar da kiwon lahiya,da kuma pannin sansanin sararin samania da na daji.

Yaki , Rikici ,  Masihwa :

Waden nan kassahi na ci ma al'uma mutunci tare da hallakar da su. Su na zaman babbar aloba, kazamar masihua ga rayuar dan adam, missali ma ga rayuar mata da yara. Karuar saye da saidawar kayan yaki, na kauda zaman lahiya da lumana a sassa da dama cikin fadin duniya, tare da tabarbarewar siasa da kuma tattalin arziki.

Wan'nan usula na kire ga jama'a domin :

- bada goyon baya ga dauken matakai waden da ke bada damar zaman lahiya ,da kuma aje makaman yaki
- bada goyon baya ga dauken matakai domin tsaida sarafa makaman yaki,da kuma yin anfani da su,ko gwadon su.
- bada goyon baya ga shirye-shiryen jama'a domin kawo kwanciar hankali da zaman lahiya, missali ma ga kasashen da ke fama da yakin kare dangi.
- kar a bada goyon baya ga ma su dauken yara tamkar sojojin yaki,da ma su wa mata hiade da kuma gana ma su azaba ko kashe su tare da yaran su.
- kar a bada goyon baya ga ma su anfani da kassa (bayan mallakar ta) tamkar abin ciwa mutunci.
- a bada goyon baya domin fararen hula su shugabanci aikace-aikacen agaji.

- a tambaya da kotin kolin majalisar dimkin duniya, y azan ki anfani da cikakkar democratia.
- ya kamata majalisar dimkin duniya,da kuma kasashe ma su arziki,su daina sawa takunkumi ga sauren kasashe,domin yin hakan na kuntatawa rayuar jama'a.
- a kuma bada goyon baya ga matakan da al'uma ke dauka domin kawo zaman lahiya da lumana cikin garurua, karkara, ko jaha.
- bada goyon baya ga dauken matakan da ke zaman rigakahin rikici, ko na hin karhi
- bada goyon baya ga dauken matakan da ke kare duk wata masihwa tare da abubuan da ta ke haddassar wa.

Pannin Kiwon Lahiya Daidai Ga Ma Su Anfani Da Shi:

Wan'nan usula na kira domin jama'a ta lara da makaraban kiwon lahiya (magunguna da sauren su) ba tare da nazarin karhin bian su ba. Da a bada damar gudanar da ka'idodin tahiar da wan'nan panni bisa cikakkar democratia da kuma ware ishashen kada-kadarin da zai bada damar shawo kan matsalolin

wan'nan usula na kire ga jama'a, da :

- da su kiye ma duk wata siasa (ta cikin kassa ko tsakanin hasashe) da ke borin maida makaraban kiwon lahiya tamkar kayan kassua.
- da gwamnatoci, su bunkassa ma'aikatun kiwon lahiya da na bada horo(lacole), da su kebe ishash'shiar dukiar da ke iya ba su damar gudanar da aikin su domin bian bukatun jama'a. Yin hakan na iya kawo sulhu ga kiwon lahiya.
- gwamnatoci,su dauki niya su kuma matsa kaimi domin gudanar da kyew-kyawar siasar kiwon lahiya; da kuma hanyoyin lara da magunguna day a kamata jama'a ta dace.

- gwamnatoci,su kiyaye saida ma'aikatun kiwon lahiya, su kuma kula da abubuan da ke farua wajen ma'aikatu ko campanai ma su zaman kan su a cikin kowace kassa,tare da sauren kungioyi.
- ya kasance,an samu sauyi ga shirye-shiryen kungiar kiwon lahiya ta duniya,domin bian bukatun matalauta.Ya kamata ta zan ki kira ga kugioyin jama'a waden da su ne cibiar al'uma domin sanin abin da ya wajaba da kuma dauken mataki na gari. Ya kuma kamata kungiar,ta tsame hannun ta daga hada-hadar yen kassua.(neman riba).
- da a bada goyon baya ga duk abubuan da ke kara ma jama'a karhin cinma gurin su domin kyewtata rayuar su.
- da a bada damar bunkassa anfani da magungunan galgajia tare da na likitoci
- da a zan ki kawo sauyi game da horon likitoci,domin ba su damar sannin,da kuma dauken matakan shawo kan matsalolin da su ke gabata. Yin hakan na kuma ba su damar aiki tare da al'uma.
- ya kasance,dubarun kiwon lahiya,da na magunguna na daidai ga bukatun jama'a.
- duk wani nazari bisa kiwon lahiya (ko da na sannin assili ne), da na kirkiro magunguna, na wakana domin bian bukatar jama'a. Nauyi ya rataya ga hukomomin da ke gudanar da wan'nan nazari,da su baiwa jama'a haske bisa abin dake iya kai da kawo.
- bada goyon baya ga yen-cin mutane na zabba ma kan su sahihiar hanya ta zama tare da iyalen su,da kuma zabbar hanyar da su ke so wajen tsarin iyali.

Gudummuar Jama'a Domin Kawo Zaman Lahiya da Lumana cikin Duniya

Gungioyi,da sauren ma su gwagwarmaya,su ne shikashiken gudanar da kyew-kyawar siasar da ke kumshe da democratia. Ya kamata a kiyaye yen-cin yen kassa,da siasa,da tattalin arziki tare da al'adun galgajia. Nauyi ya rataya ga gwamnatoci,da su dauki matakan kare yen-cin kiwon lahiyar mutane,su kuma bada damar gwagwarmaya,da baiwa jama'a damar samun labarai ta kowace hanya (radio, jarida,yen jarida,tele..) da tshoma bakinta ga al'amuran siasa na yaw da gobe.

Wan'nan usula na kire ga mutane domin:

- girka kungioyi da kuma ba su goyon baya domin karhwa-hwa tushen da zai bada damar dauken matakai.
- bada goyon baya ga matakan da ke baiwa jama'a karhin kawo ta su dubara ko nazari bisa hanyoyin tahiar da ma'aikatun jama'a a kowani sashe.
- wajen pannin kiwon lahiya,a baiwa kugioyi damar halartar taron gangami na jaha,jamhuriya ko kuma na tsakanin kassa da kassa.
- bada goyon baya ga dubarun da al'uma ke kirkirowa domin kawo ta su gudummua. Yin hakan na baiwa mutane damar tahiar da aikin cudani a duk fadin duniya.

Majalisar kiwon lahiya da Usula:

Yaw da shekaru goma da su ka huce,batun majalisar kiwon lahiya ya huskanci gardame-gardame ko kuma tantamnawa. A shekara ta dubu daya da dari tara da tassa'in da takwas,waden su kungioyi sun watsa shirin girka majalisar , da kuma shirya babban gangami na kasashe da kasashe a kassar Bangladesh, a karshen shekara ta dubu biyu. Aikace –aikace da dama sun gudana,hard a ma gangami cikin kasashe,da kuma nazari bisa kan al'amuran kiwon lahiya, da kuma rubuta wan'nan usula (abubuan da ta kumsa ).

Dan haka,wan'nan usula ta samo tushe daga lissahin yen kassa game da na kungioyin jama'a na duniya. An yarde ma wan'nan usula a taron majalisar a kassar Sava (Bangladesh ),a karshen watan desemba na shekara dubu biyu.

Haka,wan'nan usula na zaman babban gurin mu, babban kayan aikin mu,kuma kukan mu domin samun kyew-kyawar rayua tare da zaman lahiya da lumana cikin duniya. Kuma ta na zaman magama ko matat-tara domin cinma gurin da mu ka dauka.

Ku kasance tare da mu - Ku sa hannu ga usula

Mu na kira ga mutane da kuma kungioyi da su kasance tare da mu cikin wan'nan gwagwarmaya,mu na gayatar su da su sa hannun su da su kuma kawo ta su gudummua domin tahiar da usula.

Secretaria ta PHA :Gonoshasthaya Kandra

Nayarhat Dhaka 1344 Bangladesh

Lambar gidan waya: 277083167708335

Addreshin email:phasec@pha2000.org

Internet: www.pha2000.org

Fassalin ashirin ga watan January na shekara dubu daya da daya.